# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tsabta
## Kashi na goma: Al’ummominmu

Wanda ya rubuta: Nkoji C. Muhoho
Wanda ya tace: Maja Braun
Wanda ya fassara: Kabir Isa Jikamshi

**’Yan wasa:**

Sama’ila: ɗan shekara 17
Hadiza: ’yar shekara 15
Bilkisu: ’yar shekara 40
Mariya: ’yar shekara 43
Adamu: ɗan shekara 36
Dokta Husaina: ’yar shekara 34
Shugaba: ɗan shekara 60
Shugaban makaranta: ɗan shekara 45

**MAI GABATARWA:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin kashi na goma kuma na ƙarshe a cikin jerin shirye-shiryenmu na "Ji Ka Karu" a kan yaƙi da cutar gudawa. Ta irin labaran da muka ji dai, Sama'ila da Hadiza sun koyi abubuwa masu yawa a game da alamomin cutar da abin da yake haddasa ta, matakan yin rigakafin kamuwa da kuma na magance ta idan mutum ya kamu. Za mu ji yadda Sama'ila da Hadiza a yau da kuma sauran 'yan gidansu za su yada ilimin da suka koya a taron al'ummar gari domin tabbatar da kiwon lafiya.

**Fitowa ta 1: A gidan Mariya**

Sama'ila, Bilkisu, Mariya, Hadiza

| | |
|---|---|
| **SAMA'ILA** | Anti Mariya, muna godiya sosai dangane da wannan kyakkyawan kalaci da kika haɗa mana. |
| **BILKISU** | Mariya, Mariya! Har yanzu da ke da yaran nan kuna nan kuna kalaci? Za mu makara fa. |
| **MARIYA** | Bilkisu, shigo mana, ke ma ki yi kalaci! |
| **BILKISU** | Mariya! Adamu da matarsa Husaina za su iso nan ba da daɗewa ba. Mu yi sauri, don Allah! Mu yi sauri! |
| **MARIYA** | Bilkisu, ki zauna ki ɗan ci wani abu mana. Kina ta zumuɗin wannan taro. Ai muna da sauran lokaci. |
| **SAMA'ILA** | A gaskiya, ni ma ina ɗoki ƙwarai da gaske game da taimakon da babban jami'i yake bayarwa a cikinmu. |
| **BILKISU** | Yana da matuƙar muhimmanci mu yaɗa ilimin da muke da shi game da cutar gudawa ga sauran al'ummar gari. |
| **HADIZA** | Dole mu koya musu waƙarmu!<br><br>*Mu wanke hannuwanmu,*<br>*mu wanke hannuwanmu,* |

*mu wanke hannuwanmu*
*a yayin cin abinci.*
*Malallatan mutane*
*ba sa wanke hannu*
*a yayin cin abinci*
*da bayan sun fito*
*daga banɗaki a kullum.*

**SAMA'ILA** Ku fa, Mama da Anti Mariya, dole ne ku koyi wannan waƙa.

**MARIYA** Ni? Waƙa? Ai yara ne suke yin waƙa. Ai mu mun tsufa sosai da irin waɗannan abubuwan. Wai, su waƙa manya!

**BILKISU** Ina da wata shawara, Mariya. Me zai hana ba za mu sanya wa waƙar wani ƙarin waƙa ba. Kin ga idan yara suna rerawa, mu ma za mu iya yin waƙar. Dole ne dukanmu mu koye ta. Wane ne zai damu da wani ƙarin waƙa na asali ko kuma murya? Isar da saƙon waƙar, shi ne abin da ya fi muhimmanci.

**MARIYA** Ja! Mu je! Nuna mini yadda zan yi.

**SAMA'ILA da HADIZA** Sai Mama! Sai Mama! Sai Mama!

**BILKISU** *Mu wanke hannuwanmu*
*in za mu ci abinci*
*…*

**HADIZA** *Ha ha ha!* Mama, wannan ya yi kyau ƙwarai. Duk da yake ba a yi ƙarin waƙar dai-dai ba, amma dai an nuna basira.

**BILKISU** Adamu da Husaina sun iso. Ku taso, mu tafi!

**ADAMU** Mariya, Bilkisu, ina kwananku? Da fatan kun kammala kimtsawa domin wannan taron da za mu je.

**BILKISU** Lafiyarmu ƙalau, Adamu. Ina godiya ƙwarai cewa da kai da Husaina za ku tafi tare da mu. Bai kamata babban jami'in taron ya jira zuwanmu ba. Mu tashi mu tafi, Adamu.

## MAI BA DA LABARI

Yanzu kuma ko mene ne waɗannan iyalai za su yi? Kuma ko saboda mene ne Adamu da matarsa Husaina za su sake rufa musu baya? Ga dukan alamu an daɗe ana shirye-shirye game da hakan. Ko za mu iya yin hasashen abin da za su yi? Bari dai kawai mu ci gaba da saurarensu.

**Fitowa ta 2: A babban ɗakin taro**

Shugaba, Adamu, Bilkisu, Mariya, Dokta Husaina

| | |
|---|---|
| **SHUGABA** | Jama'a, ku saurara! Ku yi shiru! Kowa ya natsu! Baƙin namu sun iso. … Yanzu bari in kira babban jami'in kiwon lafiyar wannan yankin, Malam Adamu Abdullahi. |
| **ADAMU** | Assalamu alaikum, jama'a! … Muna godiya, Shugaba. Tawagata da muka zo nan yau, ba baƙuwa ba ce gare ku. Tana cikin jama'ar wannan yanki. Yawancinku kun san cewa, ba da daɗewa ba ne ɗiyar Bilkisu ta rasu a sanadiyyar cutar gudawa. |
| **SHUGABA** | Ayya! Allah ya ba da dangana, Bilkisu. |
| **ADAMU** | Amma mun zo nan ne, saboda za a iya kauce wa afkuwar irin wannan mutuwa. Muddin dukanmu muka yi aiki tare, sannan kuma muka ci gaba da kiyayewa da matakan kula da lafiya. |
| **JAMA'A** | Haka ne. E … kyakkyawan kiwon lafiya ... dole a tabbatar da ɗorewarsa…. |
| **BILKISU** | Mariya! Kai! Jikina ko ya yi sanyi ƙwarai. Mai yiwuwa wannan ba shawara ce ko mai kyau ba. |
| **MARIYA** | Haba Bilkisu, kome zai tafi daidai. Ko kina son wata uwa ta sake rasa wani ɗan ko 'yar? A'a! |
| **ADAMU** | Yanzu bari in kira Bilkisu domin ta tofa albarkacin bakinta. |

**MARIYA** Ba wani abu, je ki mana, Bilkisu, suna jiranki!

**BILKISU** Na gode, na gode ƙwarai da gaske! Mai girma Shugaba, ina godiya da ka gayyace ni zuwa wannan wurin. 'Yata Fati ta rasu a sanadiyyar cutar gudawa. Kuma tun daga lokacin, ni da sauran iyalina, da ƙawata Mariya, mun koyi abubuwa masu yawa game da cutar. Da a ce mun san abin da muka sani yanzu kafin wannan rashin, mai yiwuwa da har yanzu 'yata Fati tana nan a raye. … A da ba mu san cewa ya kamata mu riƙa jefar da ƙunzugun yara da mun gama amfani da ita nan take ba. Ya kuma kamata mu riƙa wanke hannuwanmu a ko da yaushe! Ku tuna fa cewa, a da ba ma yin duka waɗannan abubuwan.

**MAI BA DA LABARI**

Bayanai daki-daki, haka Bilkisu ta shaida wa taron irin abubuwan da ta sani game da cutar gudawa. Sai dai kuma faɗa da fatar baki kaɗai ba zai iya kawad da cutar ba, akwai buƙatar a yi aiki da shi. Wannan gidan iyali da abokansu suna son sauran al'ummar garin su koyi hanyoyin da za su kula da lafiyarsu. Yanzu lokaci ne da za a fara aiki. Don haka, bari mu karkata ga Dokta Husaina da mijinta Adamu, domin su yi wa mahalarta wannan taron bayani game da hanyoyin da za a bi domin tabbatar da zama cikin ƙoshin lafiya.

**DR HUSAINA** Na gode, na gode! Jama'a, maza da mata da mai girma Shugaba! A matsayina na likita zan faɗa muku wani abu. Akwai mace-mace masu yawa da suke wakana, waɗanda bai kamata a ce ana yinsu ba. Kowane daga cikinku zai iya nisantar samu da yaɗa ƙwayoyin cutar da suke haddasa cutar gudawa. Da farko, za mu fara da yin magani ga dukkan mutumin da ya kamu da cutar daga cikinku. Ya Shugaba, muna buƙatar wani shiri.

| | |
|---|---|
| **SHUGABA** | Wane shiri ne, Dokta Husaina? |
| **DR HUSAINA** | Mijina Adamu da ni, mun tsara cewa, za mu shirya wani aikin yin gwaji na ganin dama ga dukkan yara da manya, domin a gano ko mutum yana ɗauke da ƙwayar cutar gudawa. Daga nan kuma sai a bai wa mutane magani a asibitin gwamnati. |
| **SHUGABA** | Mun gode, mun gode! Godiya muke yi, Dokta Husaina! A gaskiya Adamu ya yi sa'a a matsayinsa na maigidanki! Amma kuma hakan ba zai nisantar da cutar gudawa ba. Ko zai yi? |
| **ADAMU** | A'a, ba zai yi ba. A saboda haka ne, ya sa muke son mu yi wasu ayyuka dabam-dabam a wannan yankin. Yara su ne suka fi zama cikin hatsari. Muna tare da Sama'ila da Hadiza, waɗanda tuni suka fara wasu ayyuka na yin rigakafin cutar gudawa a makarantarsu. |
| **MARIYA** | Adamu! Adamu, ka manta da ni! Ni ma ina son zan taimaka, in ba da tawa gudummawar. |
| **SHUGABA** | O'o, kai! Su Malama Mariya, har yanzu dai ba ki canza ba. A ko da yaushe kina son a san kina wuri. Ina matuƙar farin cikin cewa kina dai tare da mu! |
| **MARIYA** | Ni Mariya da taimakon abokiyata Bilkisu mun shirya cewa za mu riƙa yin taro da dukan iyaye mata aƙalla sau ɗaya kowane wata, inda za mu yi musayar shawarwari game da hanyoyin da za mu iya yi wa abincinmu da kuma gidajenmu rigakafi daga ƙwayoyin waɗannan cututtuka. |
| **SHUGABA** | Da kyau ƙwarai da gaske, Mariya. Ya kamata a fara waɗannan tarurruka tun daga gobe! Yanzu kuma gare ka Adamu, yaya batun yara kuma fa? Ta yaya Sama'ila da Hadiza za su iya taimakawa? |

**MAI BA DA LABARI:**

Shakka babu, ta yaya matasan za su iya taimakawa? Domin kuwa, da ma yara sun fi kasadar kamuwa da ƙwayoyin cutar. Yara suna son su taɓa kome da hannunsu zai iya kaiwa gare shi. Sukan kuma sanya hannunsu cikin baki kusan ko da yaushe. Haka kuma, yara ’yan makaranta kusan ko da yaushe suke cuɗanyar jiki da junansu. A saboda haka ne, adadin yaɗa ƙwayar cutar da ke haddasa cutar gudawa yake da yawa a cikinsu. Wannan shi ne ya sa ayyukan makaranta suke da matuƙar muhimmanci. Sama’ila da Hadiza sun fahimci haka, kuma da goyon bayan shugaban al’ummar gari da iyalan waɗannan matasa, za su duƙufa wasu shirye-shiryen taimaka wa yara.

**Fitowa ta 3: Ofishin shugaban makarantar Sama’ila**

Shugaban makaranta, Adamu, Dokta Husaina, Sama’ila, Hadiza

**SHUGABAN MAK.** Adamu da Dokta Husaina, a matsayina na shugaban wannan makaranta, ina nuna godiya da farin cikina dangane da ayyukan da kuke yi da mu.

**ADAMU** Ba kome, Hedimasta. Dole ne dukanmu mu yi aiki tare. Matata tana son irin wannan manufa da aka sanya a gaba.

**DR HUSAINA** Kwarai! Amma kuma ya kamata a yi yabo na zahiri, a yi shi ga waɗannan matasan guda biyu, Sama’ila da Hadiza. Su ne suka fara ƙirƙiro shawarwarin, inda daga bisani suka jawo mu a ciki.

**SHUGABAN MAK.** Sama’ila, Hadiza, kun san cewa, muna matuƙar alfahari da ku. Wannan aikin na dabarun kula da wuraren bayan-gida na makaranta, yana yin alfalu gaya. Kun zama manyan abubuwan koyi ga sauran ɗalibai.

**SAMA’ILA da HADIZA** Mun gode, Malam, muna matuƙar godiya!

**SAMA’ILA** Malam! Ai muna da wasu ƙarin shawarwarin.

**SHUGABAN MAK.** Sama'ila, ina saurare.

**HADIZA** Muna da wata waƙa da muke son koya wa dukannin 'yan makarantar.

**SHUGABAN MAK.** Wata waƙa?

**SAMA'ILA** E, wata waƙa ce muka shirya ni da Hadiza. Za mu rera muku ita.

**SHUGABAN MAK.** Wace irin waƙa kuma, Sama'ila?

**SAMA'ILA** Bari ka ji ta!

**SAMA'ILA da HADIZA**

*Mu wanke hannuwanmu,*
*mu wanke hannuwanmu,*
*mu wanke hannuwanmu*
*a yayin cin abinci.*
*Malallatan mutane*
*ba sa wanke hannu*
*a yayin cin abinci*
*da bayan sun fito*
*daga banɗaki a kullum.*

**SHUGABAN MAK.** Da kyau ƙwarai, da kyau, haziƙai. Za ku iya koya wa sauran ɗalibai gobe, a lokacin da suka taru domin jin jawabi.

**SAMAILA** Ai Malam, akwai wasu abubuwan…

**SHUGABAN MAK.** Wata waƙar?

**SAMA'ILA** Ba waƙa ba ce, wani aiki ne. Muna tunanin cewa za ka iya umartar kowane yaro ya riƙa kula da wani wurin ba-haya da ke cikin garin nan.

**SHUGABAN MAK.** E, ina saurare.

**ADAMU** Hedimasta, bari in taimaka wa Sama'ila da Hadiza a nan wurin. Shawarar ita ce, tun da yake yara suna tsaftace

banɗakunansu dake nan makaranta, muna son su riƙa yin haka a gidajensu da kuma sauran wuraren jama'a.

**SHUGABAN MAK.** Wannan kyakkyawar shawara ce. Ci gaba da magana!

**SAMA'ILA** Muna son fara wani kulob.

**HADIZA** Ya kamata a ƙarfafa gwiwoyin dukan ɗalibai su shiga kulob ɗin a matsayin wakilai.

**SHUGABAN MAK.** Mene ne sunan kulob ɗin?

**SAMA'ILA da HADIZA** Kulob ɗin CTC, wato *"Clean Toilets Club".* Ma'anar kulob ɗin tsaftace wuraren banɗakuna. Kowane ɗalibi zai sa idanu a kan wurin banɗaki guda ɗaya a gida ko kuma a ƙauyensa, sannan ya tabbatar da cewa mutanen da suke yin amfani da wurin, suna tsaftace shi. Uncle Adamu zai taimaka.

**ADAMU** Zan ziyarci al'ummomin a lokacin da waɗannan matasa za su je wurinsu domin in yi jawabi. Sama'ila da Hadiza kuma za su tabbata da cewa an yi aiki da abin da za a koya.

**SHUGABAN MAK.** Da kyau, haziƙai. Da ma dukan ɗalibai kamar Sama'ila da Hadiza suke. Ni ma ina da wata shawara.

**ADAMU** E.

**SHUGABAN MAK.** Me zai hana, Adamu da Dokta Husaina, ku ma ku riƙa yin jawabi a nan sau ɗaya a wata game da muhimmancin kiwon lafiya? Ku zaɓi darasin da za ku yi magana a kai, ni kuma zan kawo ɗalibai da sauran jama'ar da za su saurara!

**DR HUSAINA** Ina jin wannan zai yi kyau ƙwarai.

**ADAMU** Idan al'amura suka tafi kamar yadda aka tsara a wannan taro, zan iya cimma burin dukan irin ayyukan da ya kamata in yi a matsayina na jami'in kiwon lafiyar jama'ar wannan gari. Dukanku, kuna taimakawa domin in ji sauƙin aikina!

**MAI GABATARWA**

Ga alama, al'ummar wannan gari sun kama hanyar zama cikin ƙoshin lafiya, wanda hakan zai taimaka su yi rayuwa ba tare da fuskantar barazanar cutar gudawa ba. Sama'ila da Hadiza sun zama jakadun raya aƙidar kula da lafiya. Wannan shi ne kashi na goma kuma na ƙarshe na shirye-shiryenmu a kan kiwon lafiya da rigakafi da kuma yaƙi da cutar gudawa tsakanin al'umma. Ana iya sake sauraron wannan shiri da ma dukan waɗanda aka gabatar a baya ko kuma aiko da tsokaci ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.

---

**'Yan wasa:**

Fatima Ahmad G/Dabino
Umma Suleiman
Sadiq Murtala Mansur
Rabi Salman
Awal Yahya Abdu
Abdullahi Sani Shu'aibu
Umma Suleiman Sagagi
Abdullahi Garba
Safiya Abdullahi